Competitive Scramble is an Evil Ingenuity: Proceedings from the International Conference on the Biography and Songs of Alhaji Abubakar Kassu Zurmi in Heroic Poetry
A Publication of the Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto



| ISBN 978-978-62480-5-9 (Print) | ISBN 978-978-62480-5-9 (Online)
DOI: https://doi.org/10.65760/kassu.i1.7 Website: www.ssu.edu.ng |Issue 1 | April 2025|

# Lokutan Gargajiya Dana Addini A Bakin Kassu Zurmi

**[1]Bashar Abdullahi,**
**[1]Mustafa Umar,**
**[1]Saifullahi Ahmad Madawaki**

[1]Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Tsangayar Fasaha, Jami'ar Jihar Sakkwato

**Corresponding Author: Bashar Abdullahi** basharabdullahigusau@gmail.com
**Lambar Waya: 07033338633**

## Tsakure

Wannan takarda tana da ƙudurin dubin lokutan gargajiyar Hausawa a cikin waƙoƙin Makaɗa Kassu Zurmi. Nazarin ya mayar da hankali ga fito da yanaye-yanayen lokutan da suka yi amo a waƙoƙin Abubakar Kassu Zurmi. Binciken ya waiwayi ayyukan magabata waɗanda suke da alaƙa da nazarin. Wasu daga cikin hanyoyin tattara bayanan da aka yi amfani da su sun haɗa da: Sauraren waƙoƙin Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi da gudanar da hira ko tattaunawa da waɗanda suke da masaniya game da nazarin da aka gudanar, sai kuma karance-karance. Maƙalar ta yi amfani da tunanin Bahaushe da ke cewa: "Akwai ruwa a ƙasa, sai ga wanda bai tona ba" a matsayin hanyar ɗora aiki. Wasu daga cikin sakamakon da aka gano sun haɗa da: Hausawa suna da tsarin lokacinsu tun kafin su cuɗanya da wasu al'ummu. Waƙoƙin Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi suna ƙunshe da al'adun Hausawa waɗanda suka shafi zamantakewarsu da kuma yanayin yadda suke amfani da lokatai. Haka kuma, Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi ya yi amfani da lokatan damina da na rani a waƙoƙinsa domin nuna matsayinsu da kuma tasirinsu a rayuwar Hausawa.

**Keɓaɓɓun Kalmomi:** Lokuta da Gargajiya da kuma Baki.

**Copyright:** *Provided that the author(s) and the source are credited, noncommercial use of the article is allowed, including printing and distribution.*

## 1.0 Gabatarwa

Abu ne sananne a wurin al'umma cewa, duniyar da muke rayuwa a cikinta tana da wasu lokatai da Mahalicci ya gina ta a kansu. Waɗannan lokatai da su ne ake tafiyar da lissafin kwanaki da makonni da watanni da kuma na shekara. Tasirn waɗannan lokatai

shi ya haifar da fahimtar yanayi ga al'umma, inda duniyarmu ta ƙasar Hausa take da yanaye-yanayen rani da na damina. Bugu da ƙari, idan aka tsira wa waɗannan yanaye-yanayen rani da damina ido, za a tarar da suna da ruwa da tsaki wajen fahimtar wasu lokatai da suke ɗamfare da su. Misali, yanayin sanyi da bazara duka suna da tushe daga lokatan damina da na rani. Wannan ya nuna fahimtar yanayin lokatai shi ne yake zama jagora wajen haƙiƙance shekaru daga lokatai, waɗanda suke zama wata alama ta tabbatar da gabaci.

Buƙatar wannan takarda ce ta fayyace lokatan da Hausawa suke amfani da su na gargajiya a cikin waƙoƙin Makaɗa Abubakar Kasssu Zurmi. Haƙiƙa tunanin wannan maƙala ya tusgo ne a lokacin da ake ƙoƙarin nuna wa al'umma irin ƙoƙarin da Mawaƙan baka na Hausa sukan yi ta fuskar rayar da duk wata al'ada ta Hausawa. Wannan dalili ya sa aka yi ƙoƙarin bayyana yadda wannan mashahurin mawaƙi na ƙasar Hausa ya shigo da lokatan da Hausawa suke lissafin lamuransu da suke aukuwa a gargajiyance. Domin ko ba komai, wannan ya tabbatar wa da duniya cewa, Hausawa suna da tsarin da suke amfani da shi na lissafi tun farar safiya. Wannan ya tabbatar da maganar Hausawa da suke cewa: "Ko da iska ta zo, ta tarar da kaba tana rawa." Haka kuma idan aka dubi azancin maganganun Hausawa da suke cewa: "Lokaci ke sallata" da wanda yake cewa: "Duniya juyi-juyi kwaɗo ya faɗa ruwan zafi" duka suna tabbatar da cewa Hausawa suna fasalta rayuwarsu ne daidai da fahimtar su da lokaci. Wannan dalili ya sa lokaci yake da muhimmanci a wurinsu, kuma shi ne ya sanya yake da gurbi a cikin adabinsu.

### 1.1 Hanyoyin Gudanar da Bincike

Bayyana hanyar da aka yi amfani da ita wajen bincike tana ɗebe shakku tare da tabbatar da nagartar nazarin da aka gudanar. A ƙoƙarin gudanar da wannan bincike an samu zarafin yin amfani da hanyoyin tattara bayanai waɗanda suka haɗa da:

i. Sauraren waƙoƙin Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi a na'urar adana bayanai ta memori ta hanyar amfani da wayar hannu.
ii. An yi ƙoƙarin karanta wasu daga cikin waƙoƙin Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi waɗanda aka wallafa a cikin Littafin Magaji (2016) *Kassu Zurmi da Waƙoƙinsa.*
iii. Binciken bai kawar da kai ga tuntuɓar ɗakunan karatu a matakan ilimi daban-daban ba, inda aka yi ido biyu da wasu daga cikin ayyukan da aka gudanar masu alaƙa da wannan nazari.
iv. Haka kuma, an tuntuɓi wasu ɗaiɗaikun masana da suke da masaniya game da al'adun Hausawa da kuma waɗanda suka naƙalci waƙoƙin Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi.
v. Nazarin ya amfana da shafin sada zumunta na *WhatsApp* wanda aka ƙirƙira da manufar yayata shirin gudamar da wannan taro.

### 1.2 Hanyar Ɗora Bincike

Ƙoƙarin magabatanmu na kaiwa na hannu gida kafin a dawo a kama na dawa, ya haifar da ɗora ayyukanmu na bincike a kan tunanin magabatanmu. Domin ko ba komai, karen da ya yi cizo da gashinsa ake magani. Irin wannan yunƙuri shi ne ya haifar da ayyukan bincike waɗanda suka yi nasara saboda ɗora su a kan tunanin magabata da suka yi. Misali, Bunza, (2019) da Bala, (2021) da kuma Adamu, (2022). Wannan ya tabbatar mana da cewa, ba wani abu ne hanyar ɗora aiki ba, face yin amfani da tafarkin magabata wajen gudanar da bincike. Sakamakon haka, wannan nazari ya yi amfani da tunanin Hausawa da suke cewa: "Akwai ruwa a ƙasa, sai ga wanda bai a tona ba." Alaƙar wannan karin magana da wannan takarda shi ne, an yi amfani da waƙoƙin baka na Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi an gano tsarin lokatan Hausawa na gargajiya. Sau da dama akan

tafi neman abu wani wuri, an manta da cewa ana tare da shi a cikin ayyukan fasahohinmu na waƙoƙin baka. Da dama daga cikin mutane, sun ɗauki waƙoƙin baka a matsayin abubuwan nishaɗi kawai, sun manta da cewa a cikin ƙira ake ɗaɗi.

**2.0 Lissafin Kwanaki a Bakin Kassu Zurmi**

Ga tsarin lissafi, yana farawa ne daga rana da dare, sai idan waɗannan abubuwa guda biyu sun haɗu suke zama kwana guda. Don haka dukkan wani abu da aka ayyana da kewayowar lokacinsa (bayan ya cinye lokacin dare da na rana) yake zama kwana. Wannan dalili ya sa makaɗa yake bayyana waɗannan lokatai guda biyu a wani wuri inda yake cewa:

Jagora : Yi sannu da kura mai bin dare,
: Yi sannu da ƙwarin ƙasa,
: ..........................................
: Mai bin dare .................
: Bari mu zo ga Isah, mui mai kiɗa,
: Yanzu tun da wata ga hwara,
: Shige wa duhu,
: Na san iya ɓarna kakai.
(Kassu Zurmi: Waƙar Isa Ɗanbuzu).

A wannan wuri, Makaɗa ya fito da yanayin kwanakin wata inda hasken wata yana kaiwa matuƙa daga kwanaki goma sha biyu zuwa sha biyar, daga nan hasken wata zai cika sosai. Daga nan ne kuma zai ci gaba da raguwa kullum har ya koma duhu ya zama yanayin daren na asali ya fita. Hausawa suna lissafi da wannan hasken na wata wajen gane lokacin da yanayin wata.

Haka ma a wani ɗan waƙa ya fito da wani yanayin dare mai ban tsoro wanda ake ganin a lokacin da sawun mutane ya ɗauke. A irin wannan yanayi ba kowa ake samu ba sai dai wasu ƙwari da kuma fataken dare. Misali,

Jagora : Sugugun daka ba sallama,
: Kaholamin dare sa karnai ciri,
: Yi sannu da kura mai ban dare,
: Yi sannu da ƙwarin ƙasa,
: Sahe duk hwaɗa da maccizai ya kai.

Makaɗa Kassu yana nuna yadda Hausawa suke kallon yanayin dare a tsarin al'adunsu wanda suke lissafin su da shi. Haka kuma ya fito da lokacin yanayin kwanaki da yini da kuma dare.

Hausawa sukan fito da lokaci ta hanyar nuna siffarsa ta al'ada, wanda kuma sananne ne ga kowa a kan sami haka. Misali, kamar dare da ake samun farkonsa ko a ce tsakiyarsa ko ma ƙarshensa. Irin waɗannan ne ake samun huturu (magariba) da sauransu.

A ɓangare ɗaya kuma, Makaɗa Kassu ya nuna Hausawa suna amfani da lokutan zamani wajen lissafin awowi (Agogo) don nuna matsayi ko lokacin dare, ko safiya, watau daga farko safiya ko rana har zuwa ƙarshen dare. Misali, Makaɗa yana cewa:

Jagora : Sha biyun dare masaassarar tat samai,
: Tun da sahe kulkin badau yam mutu.
(Kassu Zurmi: Waƙar Na Gidan Duwa).

Haka lamarin yake a waƙar da ya yi wa Nomau Namagarya inda yake cewa:

Jagora : Allah dai ya kai mu gobe da sahe,
: Karhe bakwai na sahiya,
: -------------------------------
: Yacce ina hita mai kasuwa, amma ba da sheri ba,
: Ko an hana ni da rana,
: Sai iskan shabin dare ya taso.
(Kassu Zurmi: Waƙar Nomau Namagarya).

**2.1 Lokatan Addini**

A kowane lokaci, mai fasahar waƙa ko kuma wani abu na zube, akan samu tasirn addininsa a cikin ayyukansa. Don haka a wurin masana al'ada, ba a raba fasahar mutum da addininsa. Domin a kowane lokaci akan ci karo da jirwayen abin da mawaƙi ya yi imani da shi a cikin waƙoƙinsa. Kasancewar Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi mai bin tafarkin addinin Musulunci, hakan ya yi tasiri matuƙa a cikin waƙoƙinsa. Wannan tasiri shi ne ya sanya aka ci karo da wurin da yake lissafo lokutan salla yayin da yake yabon wani tauraronsa. Ga misalin abin da Makaɗa yake cewa:

Jagora : Kashi talin gilme,
: Ban dai raina Buwai ba Gajere,
: Ku Turawa wa kuka maye?
: Buwai na Ladi kashi tahi gilme,
: Bai yi ta **Azzahar** bai yi **La'asar,**
: Bai ta **Magariba,**
: Nic ce shin tsohon mi at aniyakka?
: Tsoho ka lalace,
: Yac ce shi wai sallim mi take saku?
(Kassu Zurmi: Waƙar Buwai).

Bayyana lokacin addini a cikin waƙa ya ƙara shigowa cikin waƙar da ya yi wa wani tauraronsa mai suna Kwazo, inda yake cewa:
Jagora : Muna ciki har **Azzahar** tayi ƙato bai hwasa tahowa ba,
: Har **La'asar** ta yi babane bai hwasa tahowa ba,
: Har **Magariba** ta yi ƙato bai hwassa tahowa ba.
(Kassu Zurmi: Waƙar Kwazo).

Kassu ya fito da lokutan salloli guda uku, waɗanda Hausawa Musulmai suke auna lokaci da su. Lokatan sallolin da ya lissafo su ne, Azzahar da La'asar da kuma Magariba. Ga tsarin lamarin, kowane lokaci yana da irin nasa zamani. Duk da yake Hausawa suna da tsarin lokaci tun kafin su karɓi addinin Musulunci, kodayake yanzu sun salwanta.

**3.0 Lissafin Watanni**

Hausawa al'umma ce mai fassaha lissafin watanni. Ta la'akari da yanayi da ƙasarsu take tafiya da shi wanda ya shafi tattalin arzikinsu ta hanyoyin da aka sani na noma, da kiwo da kuma kasuwanci. Noma dai kusan shi ne babban ginshiƙin hanyar tattalin Hausawa. Don haka daga gare shi ne sauran sana'ao'isu suke samun tushensu. La'akari da yadda Hausawa suke kula ga sha'nin noma musamman yadda ya shafi rayuwarsu, don haka suke fara lissafin watannin daga lokacin ruwan sama, na ƙarshen watan ɗaya watau da ruwa ya ɗauke, daga nan za a fara lissafi. Idan aka kai kwana bakwai ɗaya har zuwa bakwai biyu, ko uku har ya kai kwanakin wata, sai a fara lissafin watan ɗaya, ya kai wata

na biyu ko uku har zuwa watan bakwai, wanda daga nan za a shiga watannin ruwa (damina). Watan takwas da tara zuwa watan sha biyu na ƙarshen damina, kuma daga nan ne idan ruwa ya ɗauke ake fara sabon lissafin sabuwar shekara kamar yadda muka bayyana a farko.

Lissafin watannin Hausawa ba sabon abu ba ne, gadajje ne tun asali, don kowane watan Hausa yana da nasa suna ko kirarin da ake iya gane shi. Wannan takarda ta dubi irin waɗannan lokutan na al'adar Bahaushe da suke cikin waƙoƙin Alhaji Abubakar Kassu Zurmi inda aka nazarci yanayin yadda yake shigo da lissafin watanni a cikinsu. Misali, idan muka duba a waƙar Sale Nagidan Goga da irin yadda suka yi da shi a lokacin da aka naɗa shi Sarkin Makaɗa na ƙasar Zurmi. Don haka ya nemi gudunmawar Sale don ya tallafa mai zai yi bukin naɗin sarauta (wasa) kuma ya karɓa masa da cewa zai ba da gudunmawar duk lokacin da Kassu yake son yin wasa, har a lokacin da hidimar buki yake da wahala ga Bahaushe, watau watan bakwai.

Don haka, duk wanda zai yi buki ko wata hidima a ƙasar Hausa ga al'ada ana yin ta ne a watan ɗaya na farkon kaka ko mai bi masa na biyu har zuwa na uku. Domin a lokacin ana cikin wadata na kayan noma da sha'anin kasuwanci, suna tafiya daidai a cikin walwala.

Watan bakwai kuwa shi ne watan da ake cikin rashi, saboda lokaci ne da rani ya yi nisa, kuma damina ba ta zauna ba. Tanadin da ake da shi ya yi nisa, har ma ana yi masa kirari kamar haka: "Watan bakwai maƙarar rani, ko babu damina da alama". Kassu ya yi amfani da wannan yanayi na al'ada inda yake cewa:

Jagora : Kun jiya mabobi da ku da masu taurar fatu kuma kiɗi,
: Wallai ina raba ku da roƙon abun ruhan na dace,
: Komi roƙon mutum ana ba shi abin da ba ya so,
: Mutune komi tsircin mutum yana cimma abin da ba ya ci,
: Abun da ni hwaɗa maku ga kai na nig gani,
: Nik kai ma Sale kuka nic ce,
: Bahago an yi man sarauta,
: Wasa hwala zani yi,
: Yac ce tayar ko watan bakwai,
: Nic ce a'a bari dai a shekara,
: Tayar ko watan bakwai shege,
: Mi naka za ta ci,
: Nic ce bari a shekara, wasarmu ta hi kyau,
: A kai gudunmawa masu kai abinci baki na Ashibi,
: In an shekar wasarmu ta hi kyau.
: Tun da sauran wata biyu nittassai da kwana,
: Nic ce wasa hwa za a yi,
: Yac ce t saurar hwa zuwa ni kai,
: Har yaz zan sauran wata guda, niz zo mai,
: Nic ce wasa hwa za a yi sauran wata guda ta taho,
: Yac ce tayas ko watan bakwai ina ruwana.
(Kassu Zurmi: Waƙar Sale na Gidan Goga)

### 3.1 Watan Huɗu

Wata ne da yake kasancewa daidai lokacin da yanayin zafi ya fara. Kassu bai bar wannan lokaci ba, sai da ya shigo da shi a cikin waƙarsa domin ya nuna yanayin yadda Hausawa suka ɗauki wannan lokaci. Makaɗa Kassu ya yi ƙoƙari wajen bayyana watannin guda biyu na lissafin Hausawa kamar haka:

Jagora : Wandara ban so gardamar ba nit ƙyale,
: Nai rogo kunya ɗari da hamsin,
: Gagare bawaki- bakwai,
: Nittahiya ta Mada wurin cin rani,
: Kun san ko ba Kassu za shi aiki nai ba,
: A a don gardamar ta watse ɗai na yi,
: Ban dawo ba sai da lokaci nat shuɗa,
: Watan huɗu ya ƙare na biyat bai hita ba,
: To, hwa,
: Ba ɗari kum domi bai isa ba.
(Kassu Zurmi: Waƙar Ina ɗaya, ina ɗaya).

Abin lura a nan Kassu ya fitar da lokacin da watan huɗu yake zuwa a lissfin Hausawa. Domin a wannan lokaci ne bayan an gama sanyi kuma zafi zai shigo sosai ba kamar idan watan biyar ya kama ba, wanda a shi ne ake yin zafin bazara sosai.

Wannan lokaci ne masu noman rogon ko dankalin da ake kira ɗan rani suke ginar shi. Watau bayan shi zuwa watan biyar, wasu suke fara sharar gona (toyi) don shirin tarbar damina mai zuwa.

## 4.0 Wasu Muhumman Watanni a Addinin Musulunci

Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi ya yi amfani da basirarsa wajen bayyana wasu watannin da suke da muhimmanci a addinin Musulunci. Da alama, Makaɗa ya yi haka ne saboda ya nuna wa al'umma muhimmancin waɗannan watanni a tsarin tafarkin addinin Musulunci.

### 4.1 Watan Azumi

Azumi wani lokaci ne da al'ummar Musulmi suke gudanar da wasu nau'in ibadu domin neman kusanci ga Allah Maɗaukakin Sarki. Wannan lokaci yakan kasance sau ɗaya a kowace shekara. Wato wata guda ne da ake gudanar da wata nau'in bautar Allah a kowace shekara. Hausawa sukan yi amfani da wannan lokaci domin ayyana wani lamarinsu na buki ko kuma wani sha'ani. Watan Azumi a al'adar Hausawa yana da tarihi, kuma bayansa ne ake samun watan sallah ƙarama da watan sallah babba da kuma watan mauludi. Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi ya kalli wannan lokaci inda yake cewa:

Jagora : Watan Azumi ya kama ana ta horon jahilawa,
: Mun zo ga Malam Audu, wanda anna Allah,
: Nic ce hwaɗa mana-----
: Ka san mara sani jaki,
: Watan Azumi ya kama,
: Yac ce to madalla tambaya daidai,
: Ku rage alhwasha ku bar batutuwan banza,
: Watan Ramadan hwa ba ya son wargi,
: To in ko ya mutu zakka kukai kuna kono,
: Yadda kowa ka gyara gobe nai.
(Kassu Zurmi: Waƙar ɗan Rufa'i).

### 4.2 Watan Sallar Layya

Kassu ya bayyana lokacin sallar layya a cikin waƙoƙinsa a wurare da dama. Hausawa suna ɗaukar lissafin lokacin na shekara ga sallar layya kamar nuna cewa, idan sallar bana ta kama ko a ce bara da sallar layya. Idan kuma an yi haihuwa ne a lokacin ɗaya ko biyu ko uku da sauransu.

Jagora : In anka zo a ba shi takarda ya tallabe ta ya duba,
: Ji ya buga kalma yac ce la'ilaha illallahu Muhammadu Rasulullahi,
: Halan Birnin Magaji sun yi halinsu,
: Ai ni ma ba ni son ganin kahirai,
: Ku yi can da su a kai su bariki,
: Ku wuce da su a kai ma Bature,
: Mai ja kaɗai ka 'yan masu Oda,
: Su samu ko sallar layya Arba'in ba su gida.
(Kassu Zurmi: Tasshi Birnin Magaji).

Makaɗa Kassu Zurmi ya shahara a wurin fitar da bayanin shekara a cikin waƙoƙinsa. Kasancewar Hausawa suna da wata al'ada ta bayyana shekarar da ake ciki da bana, wadda ta wuce kuma sukan kira ta bara yayin da wadda za ta zo kuma sukan kira da baɗi. Kassu ya yi amfani da hikimarsa wajen shigo da wannan lokaci na al'adar Hausawa inda yake cewa:

Jagora : Yaro bai san baƙin cikin tauri ba,
: Sai ya bar gidansu ran da aka yi,
: Bai san Nasara na hana zamani ba,
: Korau ya yi, ta'ada yaz zo Sakkwato,
: Yash shekara uku, yad dawo gida,
: Sun yi baki-baki da Garba na Uku,
: In ka koma dawo mana bakin ranka,
: Shekara ta koma kuma ya ƙara hali nai,
: An ɗaukai an kai shi Sakkwato,
: Namijin an yammai Oda,
: Ni ɗora tambayar 'yan zaman Aure,
: Ya kun ka ji mana horon Korau,
: Sun ka ce Kassu ba mu gane ba,
: Bari sai masu wata huɗu sun dawo.
(Kassu Zurmi: Waƙar Korau Sarkin Karman Zamfaran Zurmi).

Kassu ya nuna masanin lokutan al'adar Hausawa ne musamman lokacin da ya shafi damina ko zafi ko bazara ko sanyi (hunturu). Haka kuma al'adar Hausawa ta bayyana shekarar da ake ciki da bana da wadda ta wuce da bara sai kuma wadda za ta shi go da baɗi duka Kassu ya yi nuni da su a cikin waƙoƙinsa.

### 4.3 Bara

A Bahaushiyar al'ada idan aka ce bara ana nufin shekarar da ta wuce, amma idan shekarun sun wuce ɗaya ko biyu sai a ce bariya. A lissafin da ya wuce biyu zuwa fiye sai a ce bayirar can. Irin waɗannan lissafin yana da yawa a waƙar Kassu Zurmi.

Jagora : Nalabbo koma sai mun riga,
: Ta bara ta lalace,

: Banawa na son kiɗi, na Labbo hali ba ɗan ba.
: Lallai sha yaya adda ɗan gashi,
: Ya dai yi biɗar aure, bara sai da ya samu,
: Mai gidansa yaf faɗi,...
: A'a kakar bana ta yi kyau,
: Har ta bara mun gode.
(Kassu Zurmi: Na Labbo).

Haka kuma, a waƙar Dabo Nagidan Duwa nan ma Kassu ya yi amfani da lokacin Hausawa na al'ada, ga shi kamar haka:

Jagora : In hwaɗat muku abin da yat kyauta mai lahira,
: Buriyat can an ka yi wasa, da anka yi ya yi kalara, masassarar annabo,
: Tammatsa,
: Ta wullat ƙatta dai ta kai,
: Ta wullat ƙatta dai ta kai.
(Kassu Zurmi: Waƙar Mai Dabo Na Gidan Duwa).

**4.4 Bana**

A tunanin Bahaushe kalmar bana tana nufin shekarar da ake ciki. Irin waɗannan kalmomin a kan ji su da yawa ga waƙoƙin Kassu domin nuna lokacin da ake ciki. Misali,

Jagora : Lallai Sha-yaya adda ɗan gashi,
: Ya dai yi biɗar aure,
: Bara sai da yas samu,
: Mai gidansu yaf hwaɗi,
: A'a kakar bana ta yi kyau,
: Har ta bara mun gode.
(Kassu Zurmi: Waƙar Ɗan Gidan Labbo).

Ga wata waƙar ma ta Nalabbo ya yi irin wannan maganar mai nuna matsayin lokacin shekara kamar haka:

Jagora : Ashe ya hwaɗi gaban 'yan amin,
: Har da ni kwanana takwas gidan Alƙali,
: Na Labbo koma sai man riga,
: Ta bara ta lalace ba saura.
(Kassu Zurmi: Waƙar Nalabbo).

Har wa yau, a waƙar Basare, Kassu Zurmi yana cewa:

Jagora : 'Yan kallon wuri kuce amin,
: Wanda duk bai ce min ba,
: Damunar bana na kasai.
(Kassu Zurmi: Waƙar Basare).

Bugu da ƙari, Makaɗa Kassu Zurmi ya yi amfani lokaci yayin da yake yabon wani tauraronsa mai suna Ɗan Baran Dila.

© Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto 

Jagora : Yara duk iyakar alheri a ba da raƙumi,
: Ya ba ni dawakin haihai,
: Yac ce ba ni koma sai ma doki,
: Amma ka hanƙure gulbi ya wuce,
: A ba ka raƙumi,
: Kuma ya taimakan da raƙumi ɗan dawai.
(Kassu Zurmi: Waƙar Ɗan Baran Dila).

Ɗiyan wannan waƙa ta Kassu Zurmi suna nuna mana wani lissafin na Hausawa da yake a ɓoye ga wanda ba su ba. Musamman yadda ya nuna shekara takan bayyana wasu alamu na yanayi na shekara da yake iya zama a wani lokaci.

Hausawa suna lura ga kafa tarihi ko bayyana wasu alamomi na faruwar wani abu, don haka idan aka lura da irin waɗannan abubuwa za a ɗauke su a riƙa lissafi da su. Haka ma cewar Kassu za a ba shi doki amma ya yi hanƙuri sai gulbi ya wuce, yana nufin cewa ya yi hanƙuri har ruwan damina su wuce, kaka ta yi ana cikin walwala ta nan za a ƙara ba shi doki. Don haka wannan magana tana nuna irin lissafin shekara na lokacin damina na zuwan ruwa da wucewar sa.

**4.5 Lokaci Mai Nuna Yanzu**

Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi ya fito da wasu ɗiyan waƙa masu nuna lokaci na yanzu, kuma irin waɗannan ɗiyan waƙoƙi suna da yawa a cikin waƙoƙinsa. Domin bayar da ,misali, an tsakuro kaɗan daga cikinsu.

Jagora : Gusau su Mayana sun ga raƙumi,
: Waccen Mayana na ɗauri ba na yanzu ba,
: Mayana nan dauri ya hi ƙoƙari.
(Kassu Zurmi: Waƙar Ɗan Baran Dila).

A waƙar Isah Ɗanbuzu ma Kassu Zurmi ya yi amfani da basirarsa wajen ambato lokaci a tsarin al'adar Hausawa kamar yadda ya yi a waƙoƙin da aka ambata a baya. Ga abin da yake cewa:

Jagora : Mai bin dare,
: Bari mu zo ga Isah mui mai kiɗi,
: Yanzu tun da wata ya hwara,
: Shigo wa duhu,
: Na san iya ɓarna kukai.
(Kassu Zurmi: Waƙar Isah Ɗanbuzu).

**5.0 Sakamakon Bincike**

Wasu daga cikin abubuwan da wannan takarda ta kai ga ganowa sun haɗa da:

i. Hausawa suna da tsarin lokacinsu tun kafin su cuɗanya da wasu al'ummu.
ii. Waƙoƙin Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi suna ƙunshe da al'adun Hausawa waɗanda suka shafi zamantakewarsu da kuma yanayin yadda suke amfani da lokatai.
iii. Kassu Zurmi ya yi amfani da lokatan damina da na rani a waƙoƙinsa domin nuna matsayinsu da kuma tasirinsu a rayuwar Hausawa.
iv. Nazarin ya gano cewa, duk da yanayin waƙoƙin Kassu Zurmi na maza ne, amma hakan bai sanya ya yi watsi da wasu muhimman abubuwa da suka shafi addininsa na Musulunci ba. Misali, yakan ambato lokatan azumi da na sallar

layya da kuma sauran lokatan ibada kamar sallar Azahar da La'asar da kuma Magriba.

v. Waƙoƙin baka na Hausa tamkar wata taska ce da take adana hikimomi da al'adun al'umma.

### 5.1 Kammalawa

A ƙarshe, wannan takarda ta yi ƙoƙarin bitar lokatan da Hausawa suke amfani da su na al'ada a cikin waƙoƙin Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi. Takardar ta tabbatar da cewa, makaɗa Kassu Zurmi yana shigo da lokatan al'ada wanda Hausawa suke amfani da shi wajen lissafin kwanaki a cikin waƙoƙinsa. Daga cikin lokatan da suke fitowa a cikin waƙoƙin Makaɗa Kassu Zurmi akwai kwanaki da watanni da kuma tsarin shekara na bana da bara da kuma baɗi. Kassu ya yi la'akari da cewa, akwai lokatai na dare da rana, don haka ya riƙa amfani da su a cikin waƙoƙinsa. Har wa yau, Kassu ya yi la'akari da cewa, mafiya yawan Hausawa Musulmi ne, hakan ya sanya ya yi amfani da lokatan sallolin Azahar da La'asar da kuma Mangariba. Haka kuma ya yi amfani da watannin wasu ibadu na addinin Musulunci kamar watan azumi da na sallar layya da sauransu. Haƙiƙa, Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi ya tabbatar wa da duniya cewa, Hausawa suna gina tsarin zamantakewarsu a kan lokatai, saboda haka suka yi tasiri a kan ayyukansu na yau da kullum.

### Manazarta


Adamu, S. (2022). "Jaki a Rayuwar Bahaushe." Kudin Digiri na Biyu (M.A). Sakkwato: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Danfodiyo.

Alhassan, H., Musa, U.I. da Zarruƙ, R. M. (1982). *Zaman Hausawa Bugu na Biyu.* Lagos: Islamic Publication Bureau.

Bala, I. (2021). "Gudunmawar Malaman Kusfa Zariya a Fagen Ilimi da Magunguna a Al'ummar Hausawa." Kundin Digiri na Biyu (MA). Sakkwato: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Danfodiyo.

Bunza, A. M. (2006). *Gadon Feɗe Al'ada.* Lagos: Tiwal Publications Limited.

Bunza, A. M. (2018). "Mathematical Heritage in Hausa Number System (A Proposal for Teaching Mathematics Using Nigerian Languages)." Unpublished Paper, Presented at the Seminar Series Organized by the University Research Centre, Federal Universiy, Gusau, Zamfara State at the ICT Twin Theatre.

Bunza, A. M. (2019). Kwarya a Farfajiyar Adabi da Al'adun Bahaushe. Cikin *East African Scholars Journal of Education, Humanities and Literature*, *2* (12), 720–727. ISSN 2617-443X.

Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya (2006). *Kamusun Hausa na Jami'ar Bayero.* Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Gusau, S. M. (2013). "Dangantakar Waƙoƙin Baka da Al'adun Hausawa: Bunƙasa ko Koma-baya." Cikin Bunza, A. M. et al (editoci). *Taɓarɓarewar Al'adun Hausawa (Deterioration of Hausa Culture) Pp. 761-774.* Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Kabakawa, B.U. (2012). "Mahangar Makaɗan Baka Dangane da Tattalin Arziƙin Hausawa." Kundin Digiri na Biyu (M.A). Sakkwato: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Ɗnfodiyo.

Kumbashi, I. N. (2018). "Adabi Madubin Al'ada: Tsokaci a kan Al'adar Baƙunci a Adabin Hausa." Kundin Digiri na Biyu (M.A). Sakkwato: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Magaji, A. (2016). *Kassu Zurmi da Waƙoƙinsa.* Ibadan: Spectrum Books Limited.

Sanyinnawal, S. I. (2015). "Jirwayen Sana'o'in Gargajiya a Adabin Bakan Bahaushe." Kundin Digiri na Biyu. Sakkwato: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Yunusa, Y. (1989). *Hausa a Dunƙule.* Kano: Maɗaba'ar Trium, Gidan Sa'adu Zungur.